# Wasan Banza

**Other Writers**

Aisha Umar Tsiga; Abdulamlik Garba; Abdulkadir Musa; Abubakar Ibrahim; Abubakar Usman Zumo; Adamu Inuwa Girei; Ai Philip; Aisha Ayubba Adamu; Efadah Udoh; Emmanuel Bitrus Tumba; Hadiza Alkasim; Hadiza Salihu Koko; Mahmud Ballah; Maryam Abdulkadir; Maryam Ali Galadima; Mikailu Ibrahim; Nura Jamilu Musa; Pwakuleino Maxwell; Rene Gomis; Samuel B. Bello; Shehu Halilu. Sulaiman B. Musa; Summayat Ibrahim Gambo; Zakari Mohammed Hassan; Lydia Onuoha; Bilyaminu Bello Inuwa

Hausa
Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su.

**Grace Malgwi**
Writing Trainer/Collection Editor

**Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa**
Hausa Language Consultants

**Nas Yakubu**
Bloom Trainer

**Story Writers**
Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi

Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0
Copyright:  SIL International 2009



Akwai wani yaro mai suna Baƙo.

Baƙo ba ya da tausayi.

Yana son wasan banza.



Wata rana Baƙo ya ga wani makaho.

Makaho ya ɓata hanyar gida.

Makaho ya roƙi Baƙo ya taimake shi.



Baƙo ya kama sandar makaho.

Ya kai makaho cikin daji.

Baƙo ya gudu ya bar makaho.



Ashe baban Baƙo ya gan shi.

Baban Baƙo ya kai makaho gida.



Baba ya dawo gida.

Ya kira Baƙo.

Ya ce su tafi yawo a daji.



Baƙo da Baba sun shiga daji.

Baba ya ce su yi wasan ɓoye-ɓoye



Baba ya ce Baƙo ya rufe idanunsa.

Baba ya hau bishiya ya ɓoye.



Baƙo ya buɗe idanunsa.

Baƙo ya fara neman Baba.



Baƙo ya yi sama da ƙasa.

Bai ga Babansa ba.

Baƙo ya fara kuka.

Ya ɓata hanyar gida.



Baba ya sauko daga bishiya.

Baba da Baƙo sun koma gida.

Baƙo ya daina wasan banza.